BU African Studies Center LANGUAGE PROGRAM, 232 BAY STATE ROAD, BOSTON, MA 02215 africa@bu.edu
www.bu.edu/Africa/alp 617.353.3673

## Skit 9: Rena kama ka ga gayya

**Yazi Dogo: Ɗan hakin da ka rena, shi zai tsone ma ido. Ma'anar wannan karin maganar ne.**

| | |
|---|---|
| A: | Ab! Shegun gari. Ba ka da **nauyi**. Abincin **iska**, iska taho ki ɗauki abinki. |
| B: | Dan Allah. |
| A: | E. Mene ne? |
| B: | Na ce ma, ba na son irin wannan wasa. |
| A: | Me kake so? |
| B: | Ba na son komi. Don Allah, **shafa mini lahiya**. |
| A: | To, to. Na ji kana wata **barazana** ta banza. A! Waɗannan **tumaki**, mi zaka yi da su? |
| B: | Wai! Mene ne tsakanina da kai? |
| A: | Ba ni tumkiya guda. |
| B: | Ba na badawa |
| A: | Ba ka badawa? |
| B: | I, ba na badawa. |
| A: | Ke nan in ɗauki da ƙarfi. |
| B: | In kana iyawa. Kai ba mai **yauni** ba ne. |
| A: | To. Ka ji, ko akwai nauyin. |
| B: | Kai don Allah ka shafa mini lahiya. |
| A: | An hwaɗi. Abinci iska, iska zo ki ɗauki abinki. |
| B: | Kai! Kai! Don Allah. |
| A: | Bari in jefa ka. |

© Boston University

B: Don Allah, bari.

A: Bari shege in jefa ka.

B: Madalla. .... Tsaya .... Kaƙa?

A: Wallahi kana da nauyi. Alƙur'an kana da nauyi.

B: Faɗi ƙwarai. Kara hwaɗi in ji.

A: Kana da nauyi.

B: Yi can gaba da ni. Tattaka da ni.

A: Don Allah, ruhwa mini assiri. Wasa ce nike yi da kai.

B: To! Maido ni inda ka ɗauke ni, kuma (*dariya*). To! Aje ni in ka so. Aje ni. (*Bayan an aje shi).* Yauwa! Mai yauni.

A: I. Wallahi kana da nauyi.

B: Ashe! Kai ne mai yauni. Ina so ka gane, in ka ji ana cewa: "Rena kama ka ga gayya.", ni ke nan. Sabro mai ramar ƙeta.

A: Kwarai kwa.

B: Je ka! Ba cewa ka yi yauni gare ka ba. Ko in ƙara?

A: A'a. Bari ya isa.

B: Ai, ya gani. In ya san wata, bai san wata ba.